## **Menene Illar Gubar Hayakin Carbon Monoxide?**

Hayakin Carbon Monoxide (CO), kamar yadda kake ganin sa, a iska yake ….ba za ka iya ganin shi ba. Haka nan kuma ba zaka iya jin wani wari na shi ba, wannan shine dalilin da yasa yake da matukar wahalar ganewa. To amma duk da haka dukkanin mu muna rayuwa tare da shi don haka akwai bukatar mu san wani abu akan shi.

Ana samun hayakin Carbon Monoxide ne a sakamakon kona duk wani makamashi dake dauke da Carbon, kamar Gas, ko Petur Ko Man Butane ko Daskarren Gas Ko Man Dizel ko kwal ko taki ki kuma itace ko taba sigari. Hayakin yana kunshe ne a cikin hayaki na asali wanda bai kai ga kammala konewa ko haduwa da iskar da ake shaka ba, kuma akan same shi ne daga na'urorin da ba'a hada su yadda ya kamata ba, wadannan na'u'rori sun hada da Cooker, da na'urar zafafa gida, da kayan babbaka nama, da wuta da kuma hayakin da abubuwan hawa ke fitarwa.

Akwai illoli kala biyu da suka sha banban da juna.

**Mai tsanani  na dan lokaci ~** Shakar Hayakin mai yawa na dan gajeren lokaci**,** Idan har yana da yawa matuka, to yana iya kaiwa ga halaka, kuma ana danganta shi da mutum ya kasha kanshi da kanshi kamar dai na hayakin abubuwan hawa.

**Wanda baya gushewa** ~ Shakar Hayakin na dogon lokaci wanda ba zai kai ga hallaka mutum ba. ( Ba kasafai akan gane wannan ba ko kuma a yi maganinsa, to amma duk da haka shine wanda ya fi hadari ya kuma fi shafar mutane)

**Wace alama ce zan duba?**

Idan  kana haya ne a gidanka, to kada ka dogara da furucin mai gidan cewar baa bun da same ka ( Ka nemi ganin rahoton shekara shekara na lafiyar Iskar Gas akan na'urorin dake gidan)

1. Shin akwai wani abu day a dankare/ko datti ko daskararren hayaki/ ko akwai wari na wani abu yak one a jikin na'iurar?

2. Shin na'urar tana da kyau kuma tana aiki lami lafiya? Akwai wani solatape ko wani bututu dake reto da ke nuna na'urar tana da wani lahani? Shin sai da ta kai ka ga wanke wani wuri ko yin panti a kewayen na'urar? (Idan aka ce Na'ura tana wasa'' ana nufin tana da matsala, mai yiwuwa matsalar da ke barazana ga rayuwar mutum.

3. Wurin shigowar iska – Dukkanin na'urori masu amfani da gas suna bukatar ace wannan yan aiki sosai. Shin

4. Shin ko hayakin yana ficewa daga cikin gida ba tare da yana komawa ta wata kofar ba, ko kuma yana shiga wani dakin daban. Ka duba ka tabbatar da wurin fitar hayaki ba shi da wata illa da zaka iya gani karara. Shin bututun da ke fitar da hayakin ya kere rufin gidan?

5. Kana da na’urar gano hayakin Carbon monoxide da hukumar Birttania ta tabbatar da ingancinta, sannan an sanyata yadda ya kamata, da kuma sabbin batura?

6. Idan gidanka ne, to alhaki ya rataya a wuyanka ka tabbatar da wani Injiniya na Corgi ya duba dukkanin na’urorin ura da ke cikin gidan a kowace shekara. Lalle ba shakka akwai masu ra’ayin cewar ‘’yaya zan karawa kaina wata tsadar?’’ Ko kuma suce ‘’Me zai sa in gyara abun da bai kai ga lalacewa ba’’

7. Shin akwai wata alama ta rashin lafiya a tsakanin Iyalan ka, da alamomi irin wadannan? Wane irin lokaci yanzu haka kake dauka daga wurin aiki ko kuma ka ke jira domin ka ga likita? Shin dabbobin da ke gidanka suna wata rashin lafiya?

gabanin ka samu dammar ganin likitanka? Al’amarin yana kara dagulewa ne a cikin watannin hunturu? Illar gubar hayakin Carbon monoxide tana yin kama da cututtuka daban daban, kuma abu ne da lokutta da dama ake kuskuren ganowa, abun da ke haddasa samun tattalin arzikin dab a ya tafiya yadda ya kamata.

8. Sabbi da kuma tsaffin gidaje duka suna da hadari iri daya, kamar kuma gidan da karamar hukuma ke bayarwa ko kuma gidan da wadanda suka dauki mutum aiki suke bayarwa.

Idan ka sauya gida, to ka soma da duba lafiyar na’u’rori a gidan.

<u>**Yaya zan iya fada idan wata illar guba ta shafe ni?**</u>

**Kasalar Jiki baki daya**
**Gajiya**
**Ciwon jiki da radadi**
**Ciwon kai**
**Tashin zuciya/Amai**
**Rashin son cin abinci**
**Hajijiya/ Kai sakwal**
**Rashin fahimta**
**Rashin tsari/Dimuwa**
**Fiye da mutum guda a tsakanin iyalinka/ ko wurin aiki na da alamun da suka gushewa**
**Matsalolin da aka kasa ganesu lokacin da ake da ciki/ko matsala wurin haihuwa**
**Sai mutum ya ji garau idan ya bar wurin da ake samun matsalar**
**Rashin nutsuwa/Yawan mantuwa**
**Sauye sauye akan halayya/**
**Alamun cutar sun fi yawa a lokacin watannin hunturu**
**Mura da ta ki yin sauki**
**Idan ana bukatar karin magungunan da aka saba amfani da su akan wata cuta da ake da ita kamar Asthma**

<u>**Abun Lura**</u>**: Wadannan abubuwa ba suke nan ba. Sannan mai yiwuwa ba zaa samu alamun dukkanin wadannan cututtuka ba saboda carbon monoxide na shafar mutane ta hanyoyi daban daban. Zaka iya samun wasu alamun ko kuma kadan kawai daga cikin wadannan. Alamu ne na hannunka mai sanda kawai, idan kuma kana shakka – to kaje a duba.**

## Me ya kamata Injiniya na da Likita na su yi?

Idan na’urar da ke amfani da gas tan a da lahani, to kamata yayi Injiniyan ya bayyana dalilin da ya sa ta ke dalahani, sannan ya rubuta wannan bayani a rubutun da zaa iya karantawa. Muhimman daga cikin irin wannan bayani sune, Ayi watsi da wanann na’ura, ko ta na yoyo ko kuma hanyar fitar hayakin carbon monoxide ta toshe. Idan na’ura ba ta da inganci, to dalilin shine ba ta kona abu kamar yadda ya kamata, kuma rashin kona abu kurmus, yana da hadarin samun hayakin carbon monoxide.

Wasu Injiniyoyin suna dauke da wata na’ura mai bincike iri iri, wadda zata iya shaidawa mutum abun da ke fita daga na’urarshi. Idan zaka iya ka ajiye sakamakon da aka samu.

A bushe dukkanin cikin gidan.

Idan na’ura tana fitar da hayakin carbon monoxide, to ko da injiniya ya shaida maka ko bai shaida maka ba, ka tafi asibiti kai tsaye ka shaida musu cewar ka yi imanin ka shaki gubar hayakin carbon monoxide. Zasu bukaci su san yawan carbon monoxide da ke cikin jinin ka. Kamata yayi a dauki matsayin da kake ciki, tamkar matsayin wanda ke bukatar magani cikin gaggawa. Rabin lokacin da carbon monoxide ta ke dauka gabanin ta fita daga cikin jinni shine sa’o’i hudu. Idan yawan carbon monoxide din ya nda yawa, ko kuma ka cikin rukunin da ke fuskantar mugun hadari, to asibitin zasu iya yanke shawarar ba ka iska ta shaka. Za su yi hakan ne domin su rage yawan hayakin carbon monoxide da ke cikin jininka. Zai yi kyau idan zaka je asibiti wani ya raka ka. Idan ka na shakkar wani abu to ka dauki sunan likitan da ke yi maka magani, sannan ka yi tambayoyi idan akwai abun da baka gane ba.

Ka kwantar da hankalin ka, tare da nutsuwa.

Sannan ka shaidawa Likitan ka, watau GP, da ma’aikata masu kula da kiyaye lafiyar jamaa da kuma wadanda suka kamata.

### Wane irin lahani hayakin carbon monoxide zai iya yi?

Sannu a hankali ta kan hana kwakwalwarka da sauran muhimman sassa na jiki samun iskar shaka wadda zata kai ga ‘ya yan halittu. Sannan kuma hayakin yana dauke da wasu sauran sinadarai da ake samu wajen kona abubuwa, kamar carcinogenic, masu haddasa cutar daaji da kuma sinadarai masu nauyi da ake kira metals.
Hayakin carbon monoxide, ya kan like ne a jikin kowace kwayar halitta da ke jikinka, saboda ya lunka iskar oxygen sau 240 saukin zama a cikin jinni. Illar tana iya zama kala daban daban, sannan zata iya zama ta dun dun dun, kuma a wani lokaci ba za’a iya ganin ta ba nan take domin wasu illolin sannu a hankali suke bayyana.

Akwai masu gabatar da hujjar cewa a cikin shekaru 2 zuwa 3, ana iya kaiwa gab da samun sauki baki daya, ba tare da hayakin ya kara yin wani tasiri ba a rayuwarka. Daya daga cikin dalilin hakan shine kawo yanzu, an maida hankali ne baki daya akan hayakin na carbon monoxide shi kadai. Akwai shaidu masu dumbin yawa da ke danganta hayakin carbon monoxide da sauran sinadarai da ake samu saboda rashin konewar

makashi da abubuwar kamar Rashin Haihuwa da Bari da Hujin Lebe ko Noma da haihuwar jariri babu nauyi, da Rawar Jiki, da illa ga Zuciya da Kwakwalwa da cutar daji ko sankara da kuma wasu illoli na hayalar mutum da dai sauran cututtuka daban daban. Abun da zai haddasa wannan abu na iya zama na dogon lokaci, saboda a wasu lokuttan ba iya danganta cutar da aka samu daga baya da hayakin na carbon monoxide, don haka sai a danganta shi da wani dalilin ko kuma ace haka kwatsam ya afku.

**Masu kula da lafiya (HSE) :** Doka ta dora musu alhakin su kai rahoto tare da rubuta duk wani hadari na hayakin carbon monoxide. Ka da ka dangana idan wani ya shaida maka cewar ba hakkinsa ba ne, ko kuma idan ana amfani da layin tarho

**Kamfanin Corgi** zasu iya baka shawarar Injiniyoyi tare da amsa duk wasu tambayoyi ko kuma su duba wasu na'urorin da basa aiki..

**Kamanin Transco:** Basa aiki na duba ko akwai yoyon hayakin carbon monoxide, ko duba na'u'rori. To amma idan kana tsammanin akwai yoyo na gas to zasu iya zuwa su duba. Suna aiki a kowane lokaci, sa'o'i 24.

**Za ka iya samun lambobinsu a cikin litaffi mai dauke da lambobin waya.**

**Ka tabbatar ka ajiye ko rubuta duk wata shaida ta magana da kuka yi.**

**Shin Likita na zai san san abun da ya kamata yayi?**

Babu alamar zai sani. Likitoci ciki kuwa harda wadanda suke nazari akan illar guba basu da isassashen horo akan illar gubar hayakin carbon monoxide, ko kuma shaker sauran sinadari fiye da 200 da ake samu. Idan ma har za'aiya tabbatar da illar, to taimakon da za'aiya bayarwa bai kai matsayin daya kamata ba, a wasu lokuttan akwai jahilci da griman kai. A lokacin da ake buga wannan kasida, babu wata Magana ta illar gubar carbon monoxide a cikin jerin abubuwan da ke rubuce na NHS Direct. Akan koyawa akasarin likitoci cewar hayakin carbon monoxide ko dai ya kasha mutum ko kuma ba zai kasha ba. A karkashin ka'idojin kula da maras lafiya, ya kamata a baka shawara domin kayi zabi tare da cikakken sani, da kuma magani. Za'a iya samun karin bayani akan COSY (Yadda zaka Kiyayewa da hayakin carbon monoxide) ta hanyar zama mamba. Wadanda abun ya fi yin illa akansu sune kananan Yara, Mata masu juna biyu, baki yan kasashen waje (saboda rashin masaniya akan hakkinsu/da harshe) da tsaffi ko kuma wadanda dama suke da wani laulayi ko cuta. Abubuwan da suke kara yin tasiri sun hada yawa da kuma tsawon lokacin da aka shaki hayakin na carbon monoxide. Za'a yi amfani da dokokin bayar da taimakon farko na gaggawa ga maras lafiya, watau A B C – Hanyar shakar iska da shakar isakar da kuma yawon jinni a jika. Mai yiwuwa babu wani abu daya shafi hanyar shakar iska, to amma idan hayakin carbon monoxide ya maye gurbin iskar da ake shaka, shakar iskar ita kanta yana iya faskara, sannan kuma ba zata yi amfani ga jiki ba. Illar tana afkuwa ne a yayin da hayakin carbon monoxide ya fara shafar dukkanin 'ya 'yan halitta da ke jikin mutum, Ta kan ratsa shinge da ke tsakanin jinni da kwakwalwa da kuma mahaifa. Za ka iya yin sa'a ace asibitinka ko kuma likitanka ko wurin da ake zuwa karbar magunguna zasu iya samun na'ura mai duba abun da ake shaka, to amma idan aka gano ka shaki hayakin carbon monoxide, to bai kamata amfani da wannan na'ura ya maye gurbin yin gwajin jini ba ko kuma maganin illar. Yawan hayakin na carbon monoxide da aka shaka yana iya yin illa fiye da shan taba sigari,

kuma saboda wannan abu yana cikin gidanka ne, to ba tare da samaniya ba, tana yin kisa ne babu banbanci.

**Yaya zan iya taimakon kaina da kuma wadanda na ke kauna?**

Ka rike wannan bayani domin bayar da shi

Ka sayi na'u'rar gano hayakin carbon monoxide da aka tabbatar da ingancinta, sanna a kowace shekara ka samu injiniya da Corgi ta amince da shi domin duba na'urori masu amfani da gas.

Ka bada gudunmowar na'u'rar duba hayakin carbon monoxide ga nursery ko makaranta ko kulub na matasa ko wurin aiki ko wurin kwana da yaran ke zuwa.

Hukumar nan mai taimakon tsaffi, watau Help the Aged, zata iya taimakawa da duba lafiyar gas sannan kuma Kungiyar Energy Watch tana da wani tsari mai kama da wannan ga dalibai.

Kada ka taba toshe hanyoyin fitar hayaki daga cikin gida.

Akalla a kowace shekara, a duba maka na'u'rori masu amfani da gas sannan idan kana da budadden wuri na wutar dumama gida, to dunga share shui duk shekara shima.

Kada ka bari barci ya kwashe ka a gaban na'u'ra mai amfani da gas/ko gaban wutar da ke amfani da makamashi

Ka rubuta duk wani bayani ko ka dauki hotuna sanann ka yi tambaya idan baka farin ciki da wani abu, sannan a nemi shawara.

Gabatar da kuka. Idan baka gamsu ba da wani gyara/ko aiki da aka yi maka, to ka dage ka kuma gabatar da kukanka ga hukumar da ta dace. Ka ajiye duk wata shaida ta tuntubarsu.

**Su wanene mu sannan kuma wane buri muke kokarin cimmawa?**

Mu kungiya ce wadda ke da rajista, wadda ke kokarin fito da wanann matsala fili ga jama'a domin ka sani, abun da zai bada damar samun magani mai inganci.

Mun dauri aniyar bada shawara ba tare da goyan bayan wani bad a kuma bayani mafi inganci damu kanmu muke da shi, domin ka samu damar yanke hukuncin yadda zaka taimaki kanka. Wadanda suka kubuta daga mutuwa ko kuma wadanda suka rasa wani nasu, suna bukatar taimako akai akai da magani da kuma sanin sanin cewar akwai mai kula. Ta hanyar saurare muna iya yin kiyasin bukatar kowa da kowa tare da kokarin bayar da taimako.

Don Allah ka tuna, mu a matsayinmu na mutane, mun taba fuskantar illar gubar carbon monoxide ko mun rasa wani namu, sannan muna da iyalai, don haka muna himmatuwa domin yin bakin kokarinmu a lokacin da zamu iya tare da taimakon wadanda suka

sadaukar da kansu.

Mun dauri aniyar aiki tare da kwararru wadanda suka nuna damuwarsu da kungiyoyin kiwon kafiya da kungiyoyi har da na kasuwanci da kuma mutanen da wannan abu ya shafa a unguwanni ko a kasa ko kuma a fadin duniya baki daya domin su tunkari alhakin da ya rataya a wuyansu domin su taimaka mana mu kare KA.  Muna son mu karfafa guiwar yin aiki na gari tare da kuma nuna wadanda suke yin ko in kula da aikin da ya rataya a wuyansu.

AIRSAY ba zata amince tare da cikakken sani, ta amince da wani wanda ke samun kudi ta hanyar sayar da makamshi ko ko kuma na'urori masu amfani da makashi ya dauki dawainiyar taba. Mu na son mu rike martabar mu ta hanyar zama kungiya mai zaman kanta.

Muna marhabin da gudunmowa, taimako sannan kuma zamu duba duk wasu kasidu da aka aiko mana wadanda suka shafi wannana bu

Mun rike 'yan cin na binciken duk wani kira ta waya da aka yi mana.

**Ba nufin mu bane mu maye gurbin ma'aikatan kiwon lafiya ko Injiniyoyi ko kuma bayar da shawara ta fuskar shari'a. Don haka idan kana bukatar daya daga cikin wadannan to alhaki ya rataya a wuyanka ka samo su.**

***Don Allah ka yi la'akari da cewa COSY da kuma duk wani bayani da ke akwai akan wuraren da mambobi zasu iya samun sukuni, ba'a samunsu a wani harshe idan ba harshen Turanci ba.**